Azirfa da zinare riba ne, sai hannu da hannu, alkama da alkama riba ne, sai hannu da hannu, sha'ir da sha'ir riba ne, sai hannu da hannu, dabino da dabino riba ne, sai hannu da hannu

Daga Malik ɗan Aus ɗan Hadasan cewa shi ya ce: Na taho ina cewa waye zai canji dirhamomi? sai Ɗalha ɗan Ubaidullahi alhali shi yana wurin Umar ɗan Khaɗɗab - Allah ya yarda da su - ya ce: Ka nuna mana zinarenka, sannan kazo mana, idan ɗan aikinmu ya zo, zamu baka azirfarka, sai Umar ɗan Khaɗɗab ya ce: A'a, wallahi kodai ka ba shi azirfarsa, ko ka dawo masa da zinarensa, domin cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Azirfa da zinare riba ne, sai hannu da hannu, alkama da alkama riba ne, sai hannu da hannu, sha'ir da sha'ir riba ne, sai hannu da hannu, dabino da dabino riba ne, sai hannu da hannu".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Tabi'i Malik ɗan Aus yana bada labari cewa shi ya kasance a wurinsa akwai zinarai, kuma yana son ya canja su da azirfofi, sai Ɗalha ɗan Ubaidullahi - Allah Ya yarda da shi - ya ce masa: Ka bamu zinarenka dan na gansu! sannan ya ce da shi bayan ya yanke zai saya: Ka je Ka dawo, idan ɗan aikinmu ya zo bayannan dan mu baka dirhamomin, Umar ɗan Khaɗɗab - Allah Ya yarda da shi - ya kasance yana halarce a wurin, sai ya yi inkarin wannan nau'in na mu'amala, kuma ya yi wa Ɗalha rantsuwa akan cewa ya bada azirfar a take, ko ya dawo masa da zinarensa wanda ya karba daga gare shi, kuma ya bayyana masa sababin hakan cewa Manzon Allah - tsira da a mincin Allah su tabbata agare shi - ya ambaci cewa saida zinari da azirfa ko akasin hakan ya wajaba ya zama hannu da hannu nan take, inba haka bafa to wannan cinikin zai zama riba abin haramtawa, kuma bataccen ciniki, ba'a saida zinari da azirfa ko azirfa da zinari sai hanuu da hannu kuma karba ya tabbata, haka ba'a saida alkama da alkama ko wake da wake ko sha'ir da sha'ir ko dabino da dabino sai daidai wa daidaida awo da awo,

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5889